# "Shari'a ko Siyasa"?
## Hakkin Dan-adam da Dokokin Shari'ar Musulunci a Arewacin Nijeriya

### Kammalawa

Tun cikin shekara ta dubu biyu ne, jihohi goma sha biyu da ke arewacin Nijeriya suka fadada dokokin aikata laifuffuka a karkashin ikon kotunan Shari'ar Musulunci. Dama dai tsarin Shari'ar Musulunci ana amfani da shi a arewacin Nijeriya, inda yawancin jama'ar yankin musulmi ne. To amma, an takaita aikinta ga dokokin da suka danganci rayuwan mutum. Wato an fadada aiki da Shariar ga laifukan da suka shafi kasa. Sakamakon hada sai ya janyo matsananciyar damuwa dangane da kare hakkin dan-adam.  Ya kuma haddasar da ja-in-ja a kasar wadda dama take da bambance-bambancen adddini ga kuma kundin tsarin mulki da  ya bayyana cewa ba addinin da kasar ke bi.

Musulmi da dama sun dauki tsarin Shari'a a matasyin tsarin da ya kunshi dukkan sharudda  da dokoki da suka hada da dokokin hana aikata manyan laifuka da sauran bangarori masu nasaba da addini, al'ada da kuma zamantakewar jama'a. Akwai mazhabobi da dama, kuma a cikin kowace, akwai sabanin fahimta hukunce-hukuncen Shari'a a tsakanin wadannan mazhabobi. Kungiyar kare-hakkin dan-adam ta "Human Rights Watch" ba ta da ra'ayin musu ko gaskata shari'a kanta, ko yin katsalanda a cikin wani addini ko akida; ba mu kuma da nufin yanke hukunci ko yin bayani dalla-dalla na shika-shikan wani addini ko tafarki. Abin da ya dame mu kawai shi ne take hakkin dan-adam wanda ka iya faruwa a sanadiyyar aiwatar da tsarin kowace irin doka, a kowace kasa.

Wannan rahoto ba shi  da niyar yin nazari a kan tsarin Shari'a gaba dayanta. Rahoton ya fi mai da hankali ne akan yadda ake aiki da dokokin aikata manyan laifuka a arewacin Nijeriya, kuma ya tsamo wasu sassa na dokar, da aiki da ita, wadanda suka jawo, ko kuma

ka iya kai ga take hakkin dan-adam.[1] Wasu daga cikin tsare-tsaren sun saba wa abubuwan da Musulmai da dama ke ganin su ne ainihin dokoki da ka'idojin Shari'a, da kuma sassa na kundin tsarin mulki na Najeriya. Rahoton ya gabatar da shawarwari ga gwamnatin tarayya da jihohi don kawo gyara ga wadannan bangarorin, domin tabbatar da daidaituwarsu da yarjejeniyar lura da hakkin dan-adam ta kasashen duniya da sauran yarjejeniyoyi wadda Nijeriya ta rattaba wa hannu.

Amfani da dokoki da hukunce-hukunce da suka shafi kuntatawa da kuma kaskantarwa, musamman ta hanyar aiwatar da hukuncin kisa, da na yanke hannu, da kuma na bulala, na daga cikin manya-manyan matsalolin take hakkin dan-adam da suka shafi aiwatar da Shari'a a arewacin Nijeriya. Tun shekara ta dubu biyu, kotunan shari'a sun zartar da hukuncin kisa ga akalla mutane goma, an kuma yanke hannun fiye da dozin; ga kuma hukuncin yin bulala da ake ta zartarwa a wurare da dama na arewar.[2] Kungiyar 'Human Rights Watch' tana gaba da amfani da hukuncin kisa, a cikin kowace tsarin doka na kowace kasa, domin hakan shi ne babban take hakkin rayuwa, ga shi kuma tattare da halin keta da kuntatawa da kaskantarwa. Haka kuma kungiyar ta 'Human Rights Watch' tana tsananin nuna gaba da duk wasu horarrakin keta da kaskantarwa, wadanda wasunsu gana azaba ne, misali shine yanke hannu.

Wani abin damuwa shi ne nuna rashin girmamawa da bin doka wanda ya addabi kararraki da dama da aka kai gaban kotunan Shari'a. Daga cikin manyan laifukansu da kungiyar 'Human Rights Watch' ta tabbatar akwai rashin wakilcin lauya ga wadanda aka gurfanar, da kasawar alkalai wajen bayyana wa wadanda aka gurfanar din hakkokinsu da kuma ba su hakkokin; amincewar kotu da bayanan da aka samo ta hanyar gana azaba; da kuma rashin sanin aikin alkalan kotunan Shari'a, wanda hakar shi yake sanadiyyar ake take ka'idojin aiwatar da sharia. Al'adar nan ta samun wanda aka gurfanar da laifi, sabo

---

[1] Kungiyar 'Human Rights Watch' ba ta yi bincike kan aiki da dokokin *aikata manyan laifuka ba* ko ga mutum a karkashin Shari'a. Duk da haka, kungiyoyin sa-kai da dama sun jima suna bincike a wannan sashe, musamma don karfafa matsayin mata, da kuma ilmantar da matan dangane da hakkokinsu.

[2] Kamar yadda aka yi bayani a cikin wannan rahoto, akwai wuyar samun hakikanin yawan mutanen da aka gurfanar, ko aka yanke wa hukunci a kotunan shari'a daga hannun jami'an gwamnati. Wannan adadin an tsamo shi ne daga binciken kungiyar 'Human Rights Watch' da kuma bayanan lauyoyi a Nijeriya da kuma kungiyoyin sa-kai da sauran majiyoyi.

da ikirarin amsa laifi kawai, abu ne mai ta da hankali. Sanin kowa ne cewa `yan sanda na gana azaba domin samin bayanin tun kafin a gurfana da wanda ake tuhuma a gaban kotu, ga aukuwar cin hanci da rashawa a kotuna. Kusan dukkan mutanen da ake ci wa zarafin bayin Allah ne talakawa wadanda ba su da wani dogon sani dangane da hakkokinsu ko yadda ake gudanar da hukuncin doka. Haka kuma mutane ne marasa halin da za su dauki nauyin lauya, ko da kuwa suna sane da cewa yana daga cikin hakkokinsu. A karararrakin da kungiyar 'Human Rights Watch' ta yi bincike akansu ya zuwa yanzu, ta gano cewa zartar da hukuncin Shari'a a Nijeriya bai cika sharudan kasashen duniya ba. Hakan kuma ya saba wa hakkin wanda ake tuhuma na samun adalci a gaban kotu, abin da ba wai kawai ya sabawa yarjejeniyar kasashen duniya ta tabbatar da kare hakkin dan-Adam da Nijeriya ta rattabawa hannu ba, har ma ya saba wa sassan kundin tsarin mulkin Nijeriyar. Haka kuma wasu Musulmi suna ganin hatta ka'idojin shari'ar ma ya saba mata. Kungiyar 'Human Rights Watch' ta yi amanna da cewa da kotunan Shari'a sun bi ka'idojoin shari'a, da kuma wadanda ake tuhumar sun sami cikakken taimakon lauya, da sam ba a kai ga zartar da daya dama daga cikin hukuncin kisa da na yanke hannu ba - musamman idan aka yi la'akari da sharuddan da ke tattare cikin Shari'a na hana zartar da tsatsauran hukunci, ba kuma bisa adalci ba.

Kungiyar 'Human Rights Watch' ta kuma damu da sassan dokokin Shari'a wadanda suke nuna bambanci ga mata, a ainihin dokokin da kuma yadda ake zartar da su, tare kuma da wasu tsare-tsare da suka saba wa hakkin dan-Adam. Wasu daga cikin wadannan abubuwa ba daga ainihin shariar suka samo asali ba, sai dai daga yadda ake amfani da ita da kuma halin rashin nuna tausayin da ya biyo bayan kaddamar da dokar.

Binciken da kungiyar 'Human Rights Watch' ta gudanar kan yadda Shari'a ke aiki a Nijeriya ya gano nau'uka na saba wa hakkin dan-adam wadanda ba Shari'ar ce ta haifar da su ba, sai dai suna tsokaci ne ga yadda halin kare hakkin dan-adam yake a Nijeriyar baki daya. Misali, tsararren shirin gana azaba na `yan sanda, da tsare mutum a gidan kaso na tsawon lokaci ba tare da an gurfanar da shi ba da cin hanci da rashawa a kotuna, da sanya siyasa a harkokin zartar da hukunci; ga kuma nuna bambanci a wajen hukunta masu

aikata laifukan. Hakan yana faruwa ba wai kawai a kararrakin da ke kotunan Shari'a ba, har ma ana samun kwatankacin hakan a kotuna na zamani.

A kashin gaskiya, damuwar da kungiyar 'Human Rights Watch' take nunawa kan yadda ake zartar da hukunci a kotuna a Nijeriya bai tsaya akan bangarorin da ake aiwatar da Shari'a ba. A kudu da wasu sassan kasar, inda ba a amfani da Shari'a, akwai matsalolin take hakkin dan-adam da suke ta faruwa. Kungiyar 'Human Rights Watch' ta yi cikakken bayani akan damuwar ta a wasu rahotanni, kuma tana kan ci gaba da lura da lamuran, tare kuma da tunatar da hukumomin Nijeriya akansu.[3]

Bayani da ra'ayoyin da ke kunshe cikin wannan rahoto sun samo asali ne daga binciken watanni da dama da kungiyar 'Human Rights Watch' ta gudanar a cikin shekara ta dubu biyu da uku a jihohi biyar na arewa (Kaduna, Kebbi Kano da Neja da Zamfara), da kuma tattaunawar da ta yi da wasu mutane a jihohin nan da kuma wasu sassa na Nijeriya, wadanda suka hada da wandanda kotunan Shari'a ta zartar wa hukunci, da lauyoyi, da jami'an kotuna, da kuma jami'an jihohi da na gwamnatin tarayya, da 'yan kungiyoyin Hisbah (masu kula da aiwatar da tafarkin Shari'a), da kungiyoyin da ke fafutikar kare hakkin dan-adam da sauran kungiyoyi masu zaman kansu, da shugabannin Musumi da na Kirista, da masana, da dai jama'ar gari maza da mata wadanda aiki da shari'a ke shafa ko ya shafi na kusa da su. Yawancin wadanda aka gana da su 'yan arewa ne kuma Musulmi daga al'ummomi daban-daban, wadanda kuma ra'ayoyinsu suka bambanta dangane da lamarin Shari'ar da kuma yadda ake gudanar da ita. Mun kuma nemi jin ra'ayoyin wadanda ba Musumli ba da suka fito daga sauran sassan Nijeriya.

Saboda hayaniyar da kungiyoyin da duniya suka rika yi a lokacin da aka zartas da hukuncin kisa kan Safiya Husseini da Amina Lawal, saboda samunsu da laifin zina, kungiyar 'Human Rights Watch' ta mayar da hankali kan wasu kararrakin da ba a san da

[3] Ana iya samun wasu rahotannin na kungiyar 'Human Rights Watch' dangane da halin kare hakkin dan-adam a Nijeriya a shafukan intaneti da ke www.hrw.org

su ba sosai, wanda a cikinsu an take hakkun wadanda aka tuhuma. Sai dai jama'a basu jin labarin irin wadannan kararraki ba.

Ba zai yiwu a raba kare hakkin dan-adam da ya danganci Shari'a da kuma matsalolin da ke kawo damuwa a Nijeriya baki daya ba; rahoton nan ya dubi ire-iren matsalolin nan ta hanyar duba alakarsu da kare hakkin dan-adam. Musamman, rahoton ya yi tsokaci ga takaddamar daidaituwar Shari'a da kundin tsarin mulkin kasa, ya kuma tsamo wasu sassa na kundin tsarin mulkin Nijeriya wadanda magoya baya da masu adawa da Shari'a suka yi amfani da su don kafa hujjar ra'ayoyinsu. Rahoton kuma ya yi bayanin sanya siyasa cikin lamuran addini, wanda ya dada kamari tun cikin shekara ta dubu biyu.

Baya da jami'an gwamnati da kuma wasu shugabannin masu tattsauran ra'ayi, Musulmi, yawancin jama'ar da kungiyar 'Human Rights Watch' ta gana da su sun nuna bacin ransu dangane da yadda ake aiki da Shari'ar a Nijeriya. Da dama sun yi maraba da kafuwar Shari'a a farko-farko, kuma sun nuna amincewar su ga tafarkin Shari'a, to amma sun yi bayanin rashin jin dadinsu da yadda tsarin ya koma na siyasa a hannun jami'an gwamnati. Sakamakon hakan kuwa, in ji su, shi ne cewa a aikace ba a amfani da 'Shari'a ta gaskiya' sai dai 'Shari'ar neman kuri'a'. Sun nuna shakkunsu ga kyakkyawar anniyar jami'an gwamnati wajen kafa tushen Shari'ar, tare da koken kasawar 'yan siyasa wajen aiwatar da ingantaccen tsarin tattalin arziki da na raya al'umma, suna masu nuni da tsabar talauci da kuma rashin alkibla da suka yi kakagida a duk fadin arewacin Nijeriya.

Kungiyar 'Human Rights Watch' ba ta da wani ra'ayi akan abin da ya cancanci a kira 'shari'a ta gaskiya', amma bincikenmu ya tabbatar da cewa ana amfani da Shair'ar wajen cimma burin siyasa, hakan ya jawo karin keta hakkin dan-adam – fiye ma da wanda ke ganin akwai a cikin dokokin shari'ar.[4] Kamar dai yadda aka bayyana a cikin wannan rahoto, ba ko tababar cewa gwamnonin da suka bullo da shirin Shari'a a jihohinsu sun yi hakan ne don dalilan siyasa kawai, wato neman suna da tarin kuri'a. Ba su damu su kawar

[4] Lamuran take hakkin dan-adam dangane da dokokin suna da alaka da hakkin mata da kuma gana azabar gwale-gwale, kamar yadda wannan rahoto ya yi bayani.

da kansu ko ma su ba da umurnin a saba wa hakkokin dan-adam ba don cimma burinsu na siyasa. Sun nuna halin ko-oho ga akidar nuna tausayi da kyautatawa da Musulmi da dama suke ganin ita ce ginshikin Shari'ar, ko a tsarin zartar da hukunci ko kuma a bangaren kula da tattalin arziki.

Tun dai wajajen Shekara ta dubu biyu da biyu, aiki da Shari'ar da alamu ya yi sanyi a arewacin Nijeriya. Dokokin Shari'ar sun kafu a jihohi goma sha biyu, kana kuma kotunan Shari'ar suna ci gaba da aiki tare da zartar da hukunci; to amma hobbasar siyasa ta ganin cewa ana gudanar da Shari'ar ba-sani-ba-sabo ya rage. Jami'an gwamantin jihohi su da manyan malaman addini su ne a sahun gaban ganin Shari'a na aiki a Nijeriya sun lashi takobin tabbatar da samun nasarar aiwatar da shirin, don haka suna jin nauyin fitowa karara su ce zumudin aiwatarwa ya dan lafa. To sai dai binciken sakamakon kararraki da dama, hade da kalaman jami'an gwamnatocin jihohi da wasunsu, ya nuna 'yar cijewa wajen zartar da manyan hukunce-hukuncen tsarin, kamar hukuncin kisa, da na yanke hannu, ga kuma yunkurinsu na kauce wa rigingimu. Misali, ana ci gaba da zartar da hukuncin kisa, amma ba kasafai ba, to kuma bayan hukunci daya (wanda ya kai ga sanadiyyar rataya), dukan hukunce-hukuncen kisan da aka kammala saurarен kararrakinsu tun cikin shekara ta dubu biyu, an saki masu laifin bayan an daukaka kara. Haka kuma, an zartar da hukuncin yanke hannu ga mutane fiye da dozin biyu, amma uku daga cikinsu ne kawai aka yanke wa hannu, kuma hakan bai sake faruwa ba tun a tsakiyar shekara ta dubu biyu da daya. Kungiyoyin tabbatar da ana bin dokokin shari'ar na 'yan Hisbah da alamu sun sauko daga zumudinsu na ganin ana aiki da Shari;ar sosai da sosai. Mai yiwuwa ne matsin lambar waje da kuma sarewar jama'ar gari kan yadda ake aiwatar da shirin kafa Shari'ar ya kai ga karya gwiwar zumudin 'yan siyasa: sun fahimci cewa wayonsu na amfani da Shari'ar a matsayin sassaukar hanyar yada kwarjininsu ya ci tura a fagen siyasa, musamman domin sun yi kaurin suna a idon jama'a, wadanda akansu suka dogara wajen samun goyon baya.

Kungiyar 'Human Rights Watch' ta yi amanna da cewa lokaci ya zo da gwamnatin Nijeriya da jihohin kasar za su zauna su sake duba yadda Shari'a ke aiki, da yake an sami shekaru da dama ana gudanar da ita. Dalilan siyasa kowaddanne iri ne - wadanda aka yi

bayanin wasunsu a cikin wannan rahoto hakkin jami'an gwamnatin tarayya da na jihohi ne su ga cewa aiki da Shari'ar bai kai ga saba wa hakkin dan-adam ba. A zahiri dai, wannan yana nufin yin gyara ga sassan dokokin Shari'ar, tare da soke sassan nan da sam ba su daidaitu da kare hakkin dan-adam ba, cikinsu har da nuna banbancin jinsi ga mata. Hakan kuma yana nufin bullo da matakan da ba za su kai ga rigingimu ba, kamar ganin cewa duk wanda ake tuhuma ya san hakkokinsa, musamman hakkin ba shi lauya, tare da samar da isasshen horo ga alkalai kafin sauraran kararrakin da suka shafi aikata manyan laifuka, musamman kararrakin da suka kunshi hukuncin kisa ko na horon gwale-gwale. Ire-iren matakan gudanarwa da kuma bin ka'idoji za su taimaka sosai wajen rage rashin adalci da aka fuskanta tun shekara ta dubu biyu.[5] To sai dai, yunkurin kawo sauye-sauye a sauraren kararraki cikin dokokin Shari'ar da ke aiki a yanzu bai kamata ya gusar da bukatar da ke akwai ba ta cire sassa masu ba da damar zartar da horon keta da kuma na nuna banbanci a cikin tsarin ba.

Wannan rahoto yana kunshe da shawarwari ga kasashen duniya. Kazamar siyasar da aka sanya wajen aiwatar da tsarin Shari'ar ya janyo hankulan jama'a a ciki da wajen Nijeriya. Musamman, shari'ar Safiya Husseini da Amina Lawal, matan nan biyu da aka yanke wa hukuncin kisa sanadiyya samunsu da laifin zina, haka ya tayar da hankalin jama'ar duniya wanda ya haifar da cece-kuce. Su kansu 'yan jarida sun rika nuna rashin sani da sanya batanci a irin rahotannin da suka rika bayarwa wannan hayaniya da aka yi. Daga cikin yekuwar ta 'yan jarida akwai halin nuna jahilci, da tsame da kuma karin gishiri. Kungiyar 'Human Rights Watch' ta yi amanna da cewa irin daukar matakai na kasashen waje da na kungiyoyin kasashen duniya, da kafofin watsa labarai na duniya da ire-irensu, zai iya sanadiyar kawo sauyi ga halin kare hakkin dan-adam a Nijeriya, musamman idan an bi diddigi na sahihi. Tsame batun Shari'a a matsayin hanyar da aka fi keta hakkin dan Adam a Nijeriya, sai ya nuna tamkar babu sauran hanyoyin da ake keta hakin dan-adam a wannan kasar. Alhali akwai sauran hanyoyin keta hakkin da Adam da suke bukatar a sanya ido sosai. An hallaka dubban jama'a a rigingimu tsakanin al'ummu, ko kuma a artabun da sojin Nijeriya ke haddasarwa; kisa da gana azabar da ba bisa doka ba,

[5] Ana bukatar wadannan gyare-gyare, ba wai kawai a bangaren Shari'a ba, har a cikin daukacin tsarin gudanar da hukunce-hukunce a Nijeriya.

wadanda ‘yan sanda ke aiwatarwa ya zama ruwan dare a Nijeriya; fiye da kashi biyu cikin uku na yawan fursunoni ba a saurari kararrakinsu ba. Kungiyar ‘Human Rights Watch’ na kira ga makarantan wannan rahoto da su duba sauran bangororin keta hakin dan-adam, musamman dai matsololin kungiyoyin kare hakkin dan-adam na ciki da na waje, kamar kungiyar ‘Human Rights Watch’ suka ba da rahoton aukuwarsu a rubuce.[6]

## Shawarwari

### *Ga gwamnatin Nijeriya da hukumomin kotunanta, na tarayya da na jihohi*

- Ya kamata gwamnatin tarayya Nijeriya da na jihohinta su sake duban halin dokokin Shari’a tun lokacin da aka bullo da su, tun cikin shekara ta dubu biyu, su kuma cire sassan nan da suka saba wa yarjejeniyoyin kare hakkin dan-adam, suka kuma saba wa nauyin da ya rataya a wuyan Nijeriya a karkashin kundin tsarin mulki da kuma yarjejeniyoyin kare hakkin dan-adam din da ta rattaba wa hannu na kasashen duniya. Musamman, ya dace su soke sassan da ke goyon bayan horon keta, da na kuntatawa, da kuma na kaskantarwa, wadanda suka hada har da hukuncin kisa, da na yanke hannu, da kuma na yin bulala, da kuma sassan da ke nuna bambanci ga mata. Ya kuma kamata a ba balagaggu masoya dammar kulla soyayya ta yadda suka ga ta dace.

- Ya kamata gwamnatin tarayya ta dauki matakan ganin an bar aiki da hukuncin kisa a dukkanin dokokin da ake amfani da su a Nijeriyar. Kafin yin hakan, ya kamata alkalai su guji zartar da hukuncin kisa, da na yanke hannu, da kuma na yin bulala; sannan su ma hukumomin gwamnati su daina ba da umurnin aiwatar da horon. Ya kuma kamata gwamnonin jihohi su mai da hukuncin kisa da na yanke hannu na zaman wakafi.

---

[6] Ana iya ganin dukkan rahotannin kungiyar ‘Human Rights Watch’ akan Nijeriya a shafukan intaneti da ke www.hrw.org.

- Ya kamata a saki fursunonin da aka yanke wa hukuncin yanke hannu muddin dai sun riga sun yi zaman wakafi kwatankwacin laifin da suka yi. Ya kamata wani kwamitin alkalai mai zaman kansa ya sake duba hukuncin da aka yanke musu, ya kuma ba da shawarawarin sakinsu idan hakan ya dace.

- Ya kamata hukumomi su tabbatar cewa an sami akalla alkalai uku a kotunan Shari'a na yanki da kuma na daukaka kara, wadanda ke sauraren kararrakin aikata manyan laifuka, musamman laifukan da horonsu zai kasance na kisa ne ko na yanke hannu.

- Ya kamata alkalan kotunan Shari'a su bayyana wa wadanda ake tuhuma irin hakkokinsu a koyaushe, su kuma tabbatar an fahimce su, tare da samun amincewar wadanda ake tuhuma cewa lalle sun fahimci irin horon da za su fuskanta idan aka same su da laifi. Haka kuma, ya kamata ya zama jiki ga alkalai cewa suna shaida wa wadan da a ake tuhuma game da hakkinsu na samun lauyan da zai kare su, su kuma ba su damar dage jin kara har sai sun sami lauya. Ya kamata a tabbatar cewa akwai lauyoyin dake wakiltar wadanda a ake tuhuma a duk kararrakin da horonsu zai kasance na kisa ne ko na yanke hannu, sannan kuma ya kamata gwmnatin tarayya da ta jihohi su ba da tallafin lauya ga wadan da ake tuhuma da ba su da karfin daukar lauya.

- Bai kamata alkalai su yanke hukunci ga wadan da ake tuhuma ba, don kawai sun yi ikirarin aikata laifi. A kararrakin da ake bin bahasin yin ikirari da kuma wasu shaidu, kamata ya yi alkalai su tabbatar cewa an yi ikirarin ne ba tare da tsangwamawa ko musgunawa ba. Sam bai kamata alkalai su amince da bayanan da ake tuhumar samo su ta hanyar gana azaba ba. Su kuma fursunonin da aka samu da laifi a sanadiyyar yin ikirarin da ake tuhumar samo shi ta hanyar gana azaba, to a sake su nan take.

- Ya kamata hukumomin gwamnati da na kotuna su ci gaba da habaka shirin horar da alkalan kotunan, da kuma alkalan dake aiki karkashin sauran wasu dokokin. Ya kamata horon ya mai da hankali kan muhimmancin daraja bin ka'idoji, ya kuma kasance yana kunshe da cikakken bayanin dokokin kare hakkin dan-adam da kuma yadda ake aiki da su. Ya kamata a wayar da kan alkalai game da alkawuran da Nijeiriya ta dauka a karkashin yarjeniyoyin kasashen duniya da na nahiyoyi. Ya kuma kamata a rinka lura da yadda alkalai ke amfani da horon, a kuma dauki mataka akan alkalan da ke saba wa bin ka'idojin.

- A koyaushe, ya kamata gwamnatocin jihohi su tallafa wa al'umma wajen bin bahasi da mahawarori akan dangantakar dokokin kare hakkin dan-adam da na Shari'ar Musulunci, da dai wasu tsare-tsaren dokokin kasa, suna masu ba da fifiko kan adalci, da tausayi, da kuma kare hakkokin dan-adam dake da asali a cikin Shari'a.

- Ya kamata gwamnatocin jihohi su tsawaci kungiyoyin hisbah da su guji gallaza wa jama'ar gari, tare da kafa wani shirin lura da cewa suna bin umurnin. Idan 'yan hisbar suka kama wani da ake tuhuma da sabawa shari'a to su mika shi ga 'yan sanda nan take, maimakon su zartar masa da hukunci su da kansu. Duk dan hisbar da ake tuhumarsa da gallaza wa wanda ake tuhuma, to kamata ya yi a dakatar da shi daga aikinsa, a kuma gurfanar da shi gaban shara'a.

### *Kira ga kasashen waje da kungiyoyin kawancen kasashen duniya*

- Su ci gaba da ba da goyon baya ga Nijeriya da gwamnatocin jihohinta wajen gyara dokokinsu, domin a cire horon keta, da na kuntatawa, da kuma na kasakantarwa, da kuma sassan da ke nuna bambanci ga mata, da kuma tuhumar laifi ga saduwar masoya balagaggu.

- Su shawarci hukumomin gwamnati da na kotuna wajen tabbatar da cewa ana daraja bin ka'idoji a sauraron kararraki a kotun Shari'a.

- Su ba da goyon baya ga yunkurin kungiyoyin kare-hakkin dan-adam da kuma na mata – wato gudunmawar kudi ko makamancin haka – domin su samar da wakilcin lauya, da ba da shawara, da dai ire-iren tallafi ga wadanda ake tuhuma tare kuma da wayar da kan jama'a game da hakkokinsu a karkashin Shari'a, musamman jama'ar karkara da talakawa.

- Su kara da damuwar da suke da ita akan halin kare hakkin dan-adam a Nijeriya ya zuwa wasu bangarori, inda ake nuna sabawar da a kalla ta kai munin irin ta Shari'a. Ya kamata su bayyanar da damuwar ta su da babbar murya a daidai lokacin da suke korafin take hakkin dan-adam a karkashin Shari'a. Musamman, su shawarci gwamnatin Nijeriya da ta dauki kawararan matakan hana kisan da ba ya bisa doka da dakarun tsaro ke yi ba tare da an je kotuba da kisan da ake yi wa jama'a ta sanadiya fadan kabilanci tare da kin hukunta masu haddasa irin waddana rikice-rikice. Haka kuma ya kamata gwamnatin Nijeriya ta gyara matsalolin dake tattare da dokokin na zamani da ake amfani da su a Nijeriya, musamman dai tsare mutane ba tare bin kai'ada ba da dadewa da kotuna suke yi ba tare da yanke hukunci ba da azabtawwar da 'yan sanda suke yi wa waddan ake tuhuma da aikata laifi.